# MUSULUNCI ADDININ KOWA DA KOWA

**NA**

**Mohammad Tawfik Ahmed**

**Tarjamar**

**Habu Umar Ali (Bala)**

رسالة الإسلام دين الجميع بلغة الهوسا

بسم اللهِ الرحمنِ الرحيمِ {١}

الْحَمْدُ للّهِ رَبِّ الْعَالَمِينَ {٢} الرَّحْمـنِ الرَّحِيمِ {٣} مَالِكِ يَوْمِ الدِّينِ {٤} إِيَّاكَ نَعْبُدُ وإِيَّاكَ نَسْتَعِينُ {٥} اهدِنَــــا الصِّرَاطَ المُستَقِيمَ {٦} صِرَاطَ الَّذِينَ أَنعَمتَ عَلَيهِمْ غَيرِ المَغضُوبِ عَلَيهِمْ وَلاَ الضَّالِّينَ {٧}

Da sunan Allah, Mai rahama, Mai jinkai

Dukkan yabo sun tabbata ga Allah, Ubangijin talikai. Mai rahama Mai jin-kai. Mamallakin ranan sakamako. Kai kadai muke bauta wa, kuma gare Ka kadai muke neman taimako. Ka shiryar damu hanya madaidaiciya. Hanyar wadanda Ka yi ni'ima a gare su, ba wadanda aka yi fushi a gare su ba, kuma ba batattu ba.

Da sunan Allah Mai rahama Mai jinkai

'Yan uwa maza da mata:

- Shin kun taba lura da sabanin ra'ayi dake bayyana? Shin kun taba tunani a kan lamarin addini kuwa?
- Dangane da wannan lamarin, shin kuna sane da babban makiyin da ya mamaye dangin bil'adama kuwa? Kowa na tunanin cewa, shi ko ita ya yi imani ne da Addinin gaskiya, koda shi/ita dutse ya/ta rika a matsayin abin bauta?
- Shin ka taba la'akari da yadda masu tsattsauran ra'ayi suke tunani game da imanin su kuwa?

Na tabbata, ba shakka wadannan abubuwa, sun sha maka hankali. Wata kila ma, wadannan tambayoyi su kaika ga yanke hukumcin cewa, ingantaccen magani na wannan abu Shine, a samu wani Addini guda daya da zai hada kan bil'adama wuri daya, Addinin da duk kowa zai iya fahimtar sa cikin sauki.

Ya kamata duk wani dan-Adam ya gane da kansa - ba tare da wani yayi masa jagora ba- bukatar bin wadannan gimshikai:

1- Samun wani Allah Makadaici, Wanda ake bautawa Shi kadai (domin shirka tana iya lalata farfajiyar samaniya)
2- Wanzar da kaunar alheri a cikin mutane.
3- Imani cewa; Allah Ya aiko manzanni ne domin su karantar da wadannan tsarkakan gimshikai da suka gabata ga ilahirin bil'adama.

Idan kayi tunani akan irin wannan lamarin, zaka tambayi kanka, ko shin, wannan irin Addinin, yana nan kuwa? Amsar wannan tambayar itace: "i" kwarai kuwa, wannan Addini guda daya mai hada kan mutane ya kasance tun farkon halitta, Allah ne Ya saukar zuwa ga zababbun Annabawan Sa wadanda aka aiko wa mutane.

Allah Ya ce:

"Tabbas Addini dai a wurin Allah Shine Islama, wadanda aka bai wa littafi basu saba ba face lokacin da ilimi ya zo musu, saboda zalunci a tsakanin su, duk

wanda ya kafirce wa ayoyin Allah to lallai Allah mai saurin bincike ne" [aya ta 19 Ali-imran].

Ya sake cewa:
"Duk wanda ya riki wani addinin da ba Musulunci ba, to ba za a karba daga gare shi ba, kuma a cikin lahira yana cikin tababbu"
[aya ta 85 Ali-imran].

Ashe ke nan dukkan addinai daga Allah suke, to amma wasu mutane bisa kuskure suka rika rada wa addinai suna ta hanyar danganta su ga Annabawan da suka zo da su, ko wanne da zamaninsa.

Wannan danyen aikin shine ummul'aba'isan da ya haifar da sabani da bin ra'ayin rikau a cikin al'ummomi.

Haka kuma wannan rar-rabuwan ya sanya bil'adama mantawa da Addinin gaskiya kwata-kwata .

Wasu sun rada wa Islama suna "Mahammadiyya" domin danganta Addini ga Muhammadu kamar yadda sauran addinan ake kiransu da sunan Annabawansu, duk da cewa duk Annabawa sun tabbatar da Allah guda daya kuma sun hori mutanen su da su bauta masa shi kadai.

Koda yake ni ba mai wa'azi ba ne, amma ina jin cewa wajibi ne a gareni in bayyana a takaice ma'anar wannan Addinin, domin idan mabiyan wasu addinai da ba Islama ba suka jahilci Musulunci da karantarwarsa, saurin yanke hukumcinsu akan Musulunci zai kai su ga yiwa shika-shikan sa mummunar fahimta wacce bata da jagora.

**Islama**

Kalimar "Islama" ma'anarta; aminci a tsakanin bil'adama tare da mika wuya ga nufin Allah.

Haka kuma tana nufin aminci tsakanin mutum da kansa a hannu guda, sannan tsakanin mutum da sauran mutane a daya hannun, har ila yau, Islama na nufin tsoron Allah Madaukakin sarki.

Wadannan ma'anoni gaba daya suna cikin Alkur'ani a inda mutum zai koyi yadda zai yi wa kansa alheri da sauran mutane ta hanyar aiwatar da abin da Qur'ani yake karantarwa Annabi Muhammadu (S.A.W) Shine karshen manzo amma ba Shine kadai Annabin Islama ba.

Musulamai sun yi imani da duk Annabawan da suka gabata, sun yi imani da Annabi Ibrahim, Annabi Musa da Annabi Isa (Allah Ya yarda dasu gaba daya).

Allah Ya aiko wadannan manzanni ne domin shiryar da mutane domin cika manufar Allah da kuma rayuwa cikin jin-dadi.

Alkur'ani shine tsarkakakken Litafin Islama wanda ya kunshi karantarwa ta gaskiya na sauran Litattafan Allah masu tsarki.
Allah Ya ce:

"Mun saukar maka da Littafi mai gaskata Litattafan da suka gabace shi, kuma yayi babakere akansu, saboda haka, ka yi hukumci a tsakanin su da abin da Allah Ya saukar, kada kabi son zuciyoyin su ga barin abin da yazo maka na gaskiya, ko wani daya daga cikinsu an bashi shara'a da tafarki, da Allah Ya ga dama da Ya sanyaku al'umma guda daya, "to amma bai Yi hakan ba ", domin Ya jarrabe ku

cikin abin da Ya aiko muku, to kuyi tsere wajen alheri, zuwa ga Allah makomarku take baki daya, sannan Ya baku labari game da abin da kuka kasance kuna sabani a ciki" (Ma'ida aya ta 48).

## Imani

Musulunci ya karantar da musulmai cewa suyi imani da Allah guda daya kadai, da Mala'ikunSa, da LitattafanSa, da gaba daya AnnabawanSa, da tashi bayan mutuwa da ranar sakamako.
Allah Ya ce:

"Ya ku wadanda kuka yi imani, kuyi imani da Allah da manzonSa da Littafin da Ya saukar wa manzonSa, da Litattafan da aka saukar a gabaninsa, kuma duk wanda ya kafirta da Allah da Mala'ikunSa da LitattafanSa da manzaninSa da ranar Lahira ba shakka ya bata, bata mai nisa" (Annisa'i aya ta 136).

Musulmi sun yi imani da bam-bancin dake tsakanin alheri da sharri. Duk abin da Allah Ya halitta alheri ne, kuma koda yake ana amfani dasu ne domin neman yardar Allah, amma a karshe suna kai mutane ga jin-dadi.

Haka kuma idan aka yi mummunar amfani dasu zasu kai mutane ga sharri da nadama.

Allah Ya ce:
"Wanda ya aikata aiki na gari don kan sane, wanda ya munana kuma kan sa yayi wa, kuma Ubangijinka ba mai zalumtar bayi ba ne" (Fussilat aya ta 46).

## Allah

Musulmi gaba daya sun yi imani da Allah daya wanda Ya ke Madaukaki, Masani, Mai adalci, Mai yawan taimakon bil'adama, bai Haifa ba, ba a haife Shi ba, Shine hasken sama da kasa, Mai rahama Mai jin-kai, Shine farko, Shine karshe, Shine Madauwami, idan har Annabi Isa ya kira Allah "Uba" wannan kawai yana nufin rahama da alherin da Allah Yake tattare dasu ne, ba wai yana nufin Allah ubansa ne mahaifi ba.

## Gimshikin Musulunci

Wadannan gimshikai da zan zano wajibi ne a kan musulmai.

1- **Imani mai karfi cewa Allah Yana nan**, kuma Shi kadai Ya ke, babu abin bautawa da gaskiya face Shi.

2- **Salla**: domin tsarkake jiki da daukaka rai.

3- **Azumi**: saboda daidaita tsakaninn jiki da rai, azumi waraka ce ga jiki, kuma da inganta sansancewa da ake da shi na bukatar nagartacciyar dangantaka a tsakanin mutane, dabbobi, shuka, haka kuma zai karantar da mutane hakuri da kuma kar-karfar anniya.

4- **Zakka**: domin kyakkyawar dangantaka tsakanin masu arziki da marasa arziki, domin kuwa su masu arzikin zasu ba wadanda basu dashi kashi biyu da rabi daga cikin dari (2.5%) a ko wace shekara ta Musulunci, muddin dai sun mallaki dukiyar da ta kai nauyin 85gm na ma'aunin zinare 21. koda yake mai arziki zai biya abin da muka ambata, to amma yafi kyau su kara domin kirkin su yayi galaba. Na tabbata cewa yana daga cikin abin da ya wajaba akan musulmi, taimako da jinjina wa talaka.

5- **Haji** a makka: wajibi ne ko wani musulmi ya ziyarci makka koda sau daya ne a rayuwar sa, idan da akwai daman, in shi ko ita na da ikon zuwa makka. Musulmai basu bauta wa gunki ko Annabi. Suna sanya tsarkakan ma'anoni na Islama kuma suna gode wa Allah a nan hajin, kuma wata dama ce da zasu hadu da sauran 'yan'uwa domin karfafa dankon zumunicin dake tsakanin su.

**Babu tilas a Islama**

Alkur'ani mai girma ya karantar da mutane cewa, kada a tilasta wa wani ga yarda da wani tunani, kuma duk wani yunkuri na ta'annuti haramun ne. har wa yau, duk yake-yaken musulumci an yi sune domin kare Addinin Musulunci, amma a wasu lokuta, an samu wasu shugabanni na kasashen musulmi sun yi yaki domin neman abin duniya da cimma manufofinsu, sakamakon haka ne ma, wadannan shugabanni suka fado daga kololuwar girmar da magabatansu wadanda suka riki Addini, suka gina, ashe ke nan baza a zargi Islama ba akan wannan faduwa, domin Islama da kansa bai yarda da irin wannan yakin ba, bugu da kari, duk mabiyan sauran addinai su ma sun yi irin wannan yakin da sunan addini alhali kuwa addini ba ruwansa da wannan fadi.

Islama ya bai wa mutane cikakken 'yanci na aiki da fada aji, ta girmama ran dan-Adam ba tare da ta'addanci ba saboda shi ko ita zai rayu cikin aminci.

Domin ka zama musulmi ba kawai aikata wasu abubuwa na bauta ba ne, domin Islama ba bauta ba ne kadai, amma kuma Islama Addini ne na cikakken zaman lafiya da mutane.

Ko wane jariri daga haihuwarsa yana a matsayin musulmi.
Annabi Muhammad (S.A.W) ya ce: "kowa ana haihuwarsa ne akan "fitira" (wato 'yanci na zabi) sai dai iyayensa su mayar da shi Bayahude ko mabiyin Addinin kirista ko maras addini" [Ahmad ne ya ruwaito].

**Ni musulmi ne; Na gaji zaman lafiya**

- Na yi imani da Allah daya, Shine Mai karewa, bai a iya raba Shi ba, iliminSa kuma Yana tare damu ako ina, kuma Shi ba a kebe Yake a wani wuri ba. Allah Ya ce:

(Shi ne Ya halicci sammai da kasa cikin kwanaki shida sannan ya daidaita a kan Al'arshi, Yana sanin abin dake shiga cikin kasa da abin dake fitowa daga cikin sa, da abin dake sauka daga sama da abin dake haurawa cikinta, kuma Yana tare da ku duk inda kuke, kuma Allah na ganin abin da kuke aikatawa) [Alhadid - 4].

*Babu abin da yayi kama da Shi, kuma Shine ya halicci Dukkan komai, na yi imani da AnnabawanSa ba tare da bambanta tsakanin Musa da Isa, da Muhammadu [A.S]

A wurin Allah kadai nake neman agaji, shiriya da kuma gafarar zunubai na, kai tsaye ba tare da wani ya taimaka ba ko yayi mini sakaina, ban taba fasa kiran Allah ba, a ko wane lokaci, kuma ina jin cewa iliminSa na tare dani a duk inda nake, Shine mai hukunta Dukkan ayyuka na, kuma ina bin dokokin Sa da aka fada a cikin Alkur'ani mai girma.

Ina bin karantarwar Musulunci, salla azumi, zakka, hajji a makka.

Kisan kai da kunar bakin wake haramun ne a Islama, tunda Islama ta bukaci mutane su rayu cikin aminci.

Bana aikata zina, kuma ina kiyaye duk wata zuga da zata kai ni ga lalacewa ko bata daga hanya madaidaiciya, domin na san cewa dabi'ar zuciya da rauni take. Allah Ya na cewa:

(Kada ku kusanci zina, domin ta kasance alfasha, kuma ta munana ga zama tafarki) [Isra'i - 32].

Jin-dadi na gaskiya Shine jin-dadin da nadama bata biyo shi, irin wannan jin-dadin ana samu ne ta hanyar manyan zukata da rai take kare su.

Kyakkyawan Misali a nan Shine; mutumin da ya nufi aikata zina, amma lamarinsa bai bar shi ba, to da ya kasance a karkashin tasirin giya bai gushe ba har sai da ya kashe mijin matan yayin da mijin yayi yunkurin shiga tsakaninsa da zina da matan, ya kashe wanda ke kan gaskiya yayin da yake karkashin tasirin maye, ashe ke nan giya tana iya zama asalin duk wani laifi.

* Bana caca, ko da na dan kudi kadan ne, saboda mai caca ba ya mutunta abin dake yake samu, sanya sa'ar mutum  a kan wani abu ko wasan kati ko makamantansu abin kunya ne kuma rashin mutumci ne.

Allah Ya ce:

(Ya ku wadanda kuka yi imani, lallai giya da caca da gumaka da kiban kuri'a kazanta ne na aikin shedan, saboda haka ku nisance su ko zaku tsira) [Ma'ida 90]

Musulmi baya ba da kudi da ruwa saboda wannan hanya ce mai gadar da bakin ciki.

Idan musulmi yana da hali ya kamata ya bada bashi, kuma yana iya neman a lamince masa ta hanyar jingina domin ya tabbata kudin sa zai dawo masa, amma kuma bai halatta wanda aka bai wa jingina yayi amfani da wani abu na jingina ba.
Allah Ya ce: (ya ku wadanda kuka yi imani kuji tsoron Allah, ku bar abin da ya saura na riba in kun kasance muminai. idan baku aikata ba, to Allah Yana sanar daku yaki daga gare Shi, idan kun tuba to ku karbi uwar kudinku kadai, kada kuyi zalumci kada a zalumceku, idan wanda ya dauki bashin ya kasance a cikin tsanani to a saurara masa har ya samu yalwa, ku bar masa sadaka, shi yafi muku alheri in kun sani) [Albakara 278-280]

Musulmi baya zagin mutane ko maganganu na batsa game da 'yan'uwansa musulmai, domin duk wanda yayi da dan uwansa yana kama da wandake cin naman dan uwan sa daya mutu, wannan ya hada da wadanda suke kushe wa mutane a bayan idonsu amma baza su iya fada musu a idonsu ba. Allah Ya ce: (mummunai 'yan'uwan juna ne, ku shirya tsakanin 'yan'uwantakanku, kuji tsoron Allah ko za ku samu jin-kai. Ya ku wadanda kuka yi imani, kada wadansu mutane suyi wa wasu mutane izgili, suna iya zama mafiya alheri, haka kada wasu mata suyi wa wasu mata izgili domin suna iya zama fiye da su, kada ku aibanta kawunan ku, kada ku jefi juna da miyagun lakabobi, tir da sunan fasikanci bayan imani, wadanda basu tuba ba sune azzalumai. Ya ku wadanda suka yi imani ku nisanci yawa-yawan zato, lallai sashen zato zunubi ne, kada kuyi leken asiri kada sashen ku su yi da sashe, shin dayanku yana son yaci naman dan uwan sa alhali ya mutu? To ku ki cin, ku ji tsoron Allah, lallai Allah Mai karban tuba ne Mai jin-kai) [Alhujurat 10-12]

## Imani da aiki

Imani ba tare da aiki ba, ragagge ne, imani kadai ba zai wadatar ba muddin ba a juya shi zuwa ga aiki ba.

Musulmai sun yi imani cewa Allah Yana hukumta ayyukansu kuma sune da alhakin duk abin da zai biyo baya, ko anan duniya ko a ranar lahira.

Ko wani musulmi ko musulma zai dauki nauyin aikin sa, domin babu wani mai daukar laifin wani.

Allah Ya na cewa: (Na rantse da zamani. Lallai mutum yana cikin asara. Sai dai wadanda suka yi imani kana suka yi aiki na gari, suka yi wa juna wasiya da gaskiya kuma suka yi wa juna wasiya da hakuri.) [Al'asar 1-4]

## Islama da zamantakewa

### *Matsayin mata a Musulunci

Maza da mata daga asali daya suke kuma rai iri daya gare su, kuma Allah Ya sanya musu hankali da karfi tun ran gini tun ran zane.

A cikin Islama maza da mata suna daukar nauyi, kuma ana lura da mata cewa su suna iya jure wa rayuwa har zuwa wata iyaka. Ya kamata maza da mata suyi aiki a rayuwar su gwargwadon yadda ya dace da dabi'arsu.

Abin da yafi dacewa ga matan musulmi shi ne ta bi mijin ta, kuma a matsayin ta na uwa Shine ta kula da 'ya'yanta, abin nufi Shine mace tayi amfani da yawancin lokacin ta domin tafiyarwa da kula da gidanta domin Shine aikin ta na hakika.

Haka kuma idan mace ta bukaci zuwa aiki dole ne ta kula da shika-shikan Musulunci, kuma ta zabi aikin da ya dace da dabi'arta, ga musali; karantarwa, aikin likita, ko ilimin da ke nazarin haifar jariri ko cututtukan yara da makamantan su.

Bisa la'akari da ra'ayin Islama, ina iya cewa mata sun samu mutuntawa da girmamawa a duk inda suke. Ashe ke nan idan aka yi wa mata mu'amala wace bata kamata ba, a wasu wurare a gabas ko a yamma, wannan sakamakon rashin aiki da Musulunci ne a wadannan wurare.

Allah Yace: (yana daga cikin ayoyinSa, halitta muku mata daga kawunan ku (wato bangaren jikin ku) domin ku samu sukuni da natsuwa gare su, kuma Mu ka sanya soyayya da tausayi a tsakanin ku lallai ne cikin wadancan abubuwa da muka ambata akwai ayoyi ga mutane masu tunani) [Rum 21]

## Zargin makiyan Musulunci

Ra'ayinnan na ban haushi da ake yadawa game da Musulunci a cikin litattafan marubuta masu tsattsauran ra'ayi ba gaskiya bane, hakika sun ketare gaskiya yayin da suka rungumi wannan ra'ayi na karya a rubutun su da aka watsa a daukacin duniya.

Mai kallo da idon basira ya kamata ya sanar da kansa ko kanta da farko game da gimshikin lamarin, domin ya iya gina ra'ayi na gaskiya game da ra'ayin.

A fili yake, a bayyane cewa, wadannan masu tsattsauran ra'ayi suna hidimar manufar masu mulkin mallaka ne domin sun jahilci kashin kazan da kasashen yamma suke so su goga wa kasashen gabas marasa galihu, alhalin suna karyar cewa su bauta suke yaka da taimaka ma wahalallu.

Wace gyara kasashen yamma suka kayo wa kasashen gabas? Shin sun zone domin rauna-na da lalata al'umma ta gari ta hanyar yada giya da baza karuwanci ne?.

**Daidaito da 'yan'uwantaka a cikin Musulunci**

Islama itace Addinin tauhidi da daidaito a tsakanin bil-adama domin cimma yardar Mahaliccinsu. Koda yake akwai sabanin matsayi a tsakanin mutane amma dai ya zama dole su hada guiwa kuma su samu kyakkyawan dangantaka a tsakani tare da
jinjina wa juna. Alal misali, dole masu arzaki su taimaka wa marasa arziki, wannan cudene-niya ce da ta wanzu a tsarin da ake kira tsarin rashin kymar baki.

Karkata da wariya sakamakon asali ko launi ko al'adu be da wuri a Musulunci, alhalin ana daukar mutuntaka a matsayin dangi guda wanda bakake da farare suka cakude suka zama tamakar abu guda daya: 'yan'uwantaka. Allah Yace: (ya ku mutane lallai ne Mun halicce ku daga na miji da mace kuma Muka sanya ku al'ummomi da kabilu domin ku san juna, lallai mafi daraja a cikin ku a wurin Allah Shine wanda yafi tsoron Allah, lallai Allah Shine Masani Mai labari) [Alhujurat 13].

**Cin gashin kai**

Islama ya karfafa ra'ayin daidaikun mutane kuma ta mutunta akidar kowa muddin yana cikin iyakar kya-kyawan fahimta ta Addinin gaskiya. Allah Yana cewa: (kace ni kawai da abu daya nake yi muku wa'azi, ku tashi don Allah, biyu-biyu ko daya-daya, sannan kuyi tunani, babu wata hauka game da abokin ku "Muhammadu" shi ba komai ba ne, face mai gargadi gare ku gabanin azaba mai tsananin) [Saba'a 46]

**Islama da kimiya**

Islama yayi la'akari da neman ilimi a matsayin wajibi akan duk wani musulmi. Allah Yace: (ya ku wadanda kuka yi imani, idan akace muku, ku yalwata a mazauni to ku yalwata Allah zai yalwata muku, kuma idan aka ce muku, ku mike, to ku mike, Allah zai daukaka darajojin wadanda suka yi imani da wadanda aka baiwa ilimi cikin ku, Allah Masani ne game da abin da kuke aikatawa) [Al-mujadala 11].

**Islama da aiki**

**"Ku biya ma'aikaci la'adarsa kafin guminsa ya bushe"**

Wancan magana da ta gabata an ruwaito ta ne daga manzon Allah (p.b.u.h) [Ibnu maja ne ya ruwaito].

Haka dai duk wani aiki da zai ka ga samun abin da za a rayu cikin mutunci abin darajantawa ne, tundake rashin aiki ba abu bane mai kyau. Allah Yace: (kace: kuyi aiki, da sannu Allah zai ga ayyukanku da manzonSa, sannan a mayar daku zuwa ga masanin abin dake fake da wandake bayyane, sannan ya baku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa) [Attauba 105].

**Tattalin arziki a Islama**

Ko wace gwamnati ta Islama wajibi ne ta biya wa mutanenta manyan bukatunsu: mafaka, abinci da sutura.

Tsarin Musulunci na tattalin arziki an aiwatar a cikin karnoni da dama kuma ya samu ga-garumin nasara.

Islama ta kiyaye wa ma'aikata la'adar aikinsu ba tare da la'akari da irin kokarin da suka yi ba da kuma irin dabi'ar wannan aikin.

Arzikin mutane na musumman Shine tushen duk wani aiki na masana'anta, dalilin ke nan da Islama ta darajanta arzikin mutane, sakamakon haka ne ma yasa ta kare duk wasu ababa da za su habab-baka aiki kamar yadda ta kare rayuwa.

**Gado a cikin Musulunci**

Tsabi'ar mutum ne da fitirarsa, yunkurin ganin cewa lallai ya wanzar da sunansa a bayan kasa. Wannan burin yana cika idan mutum yaga 'ya'yan sa da jikokin sa suna kare sunan sa. Don haka ne yake kokarin yi musu hidima.

Wadannan hidimomi ana ganin cewa wasu sanadarai ne masu muhimmancin gaske wajen ci gaba, kuma wasu gimshikai ne na gado. A hanu guda kuma, gado wata hanya ce ta rabon arziki ko sake rabashi a cikin Islama, domin mata da 'ya'ya maza da mata suna da rabo a cikin abin da mahaifin su ya bari. Idan mahaifin bai da da, matar sa, mahaifin sa, mahaifiyar sa, 'yan'uwan sa da 'ya'yan sa mata zasu gaje dukiyar sa, ashe ke nan rabon gado wata hanya ce ta raba dukiya memakon tara wa a wasu 'yan tsirarun hannaye abin da zai ka ga haifar da tsarin tara dukiya a wurin mutum daya. Har ila yau rabon gado yana kai ga adalci da karfafa dankon zumunci tsakanin 'ya'ya da dangi, bugu da kari, Islama tana kallon mutum a matsayin wakilin Allah wanda ya gaji arziki wanda alal hakika na Allah ne, ashe ke nan wajibi ne wakili yayi iya kokarin sa domin amfanin bil'adama.

Allah Yana cewa: (kada ku bawa wawaye dukiyar ku da Allah Ya baku damar tafiyar wa, ku ciyar dasu, ku tufasar dasu, ku fada musu magana ta girma da arziki) [An-nisa'a- 5]

Ashe ke nan wajibi ne a hana wawaye barna da dukiyoyinsu, koda yake mutum yana da 'yanci ya mallaki kadarori, amma duk da haka ana ganin cewa: dukiyar al'umma ce da ya zama dole a kare, ke nan idan musulmi yana barna da dukiyarsa, tafiyar da wannan dukiya zata koma hanu wani wakilinsa ma kusanci da zai kare wannan dukiyar.

**Kasuwanci**

Ana la'akari da kasuwanci a matsayin manyan jigogin tattalin arziki a Musulunci, domin yana gina wajen kashi 90% na hanyoyin samun riba, dalilin ke nan da ya sanya Islama gindaya tsauraran matakai domin kare gaskiya da amana a harkar kasuwanci.

Manzon Allah ya ce: "Cinikayya ana yin tane da zabi (babu tilas) sai dai idan bangarorin biyu sun rabo, idan suka yi gaskiya suka bayyana za a albarkaci cinikin nasu, idan suka yi karya kana suka boye (abin da suka sani) za a zare albarka daga kasuwancin nasu." [Buhari ne ya ruwaito].

**(Ihtikari)**
**ko kuma, tsarin yin kane-kane akan abin kasuwa**

Yin kane-kane akan abinci domin yayi tsada kuma farashinsa ya haura haramun ne a Musulunci.

Har wa yau, daga farashi haramun ne. Islama ya gindaya wasu dokoki dake tafiyar da kasuwanci na kasa da kasa ta yadda zai dace da 'yan'uwantar dake tsakanin bil'adama.

**Mummunan amfani da mutane**

Mummunar amfani da mutane ko wani iri ne an haramta shi, domin mutane su rayu cikin sauki, idan mammaci bai bar ishash-shiyar dukiya ba domin biyan bashinsa ko bashinta, wajibi ne akan gomnatin Islama ya biya wannan bashin saboda gudun rudani a harkar saye da sayarwa. Annabi Muhammadu ya ce: "Nafi mumunai kusa da kawunan su, saboda haka duk wani mumini da ya mutu ya bar

bashi to biyar sa na kaina, kuma duk wanda ya mutu ya bar dukiya to na magadan sa ne." [Buhari ne ya ruwaito].

**Riba**

Riba haramun ce a Musulunci, domin gimshikin da yace: "babu riba ba tare da wahala ba, kuma babu kudi ba tare da aiki ba"

Allah Yace: (Allah zai kwashe albarkar riba kuma zai haba-bbaka sadaka Allah ba Ya son kowane mai yawan kafirci mai yawan laifi) [Al-bakara- 276]

An kamanta maciyin riba a cikin alkur'ani da wanda "inna" ta shafe shi (aljani ya buge shi) ta yadda ba zai iya tashi ba.

Maciyin riba yana wanzuwa ne cikin son kai har abin ya kaishi ga rasa duk wani jin tausayi.

**Tsabi'ar Islama**

Islama shine Addinin da aka turo wa daukacin bil'adama a ko wane zamani, dalilin ke nan ma da yasa Islama ta sifantu da wadannan kebantattun siffofi:

1- Islama Addinin baligin mutum ne wandake rungumanta bayan tunani da amfani da kaifin kwa-kwalwa ba tare da bukatar wata gabatar wa ba.
2- Islama Addini ne da Allah Ya saukar kan duk manzanin da aka aika wa mutanen da suka bata saboda jahilcin su, rashin fahimta, da kuma bin son zuciyoyin su da kuma yunkurin da suke yi na batar da mutane.
3- Islama ya umurci mabiyanta da suyi imani da duk Annabawa da manzanni da Allah Ya aiko, ko sun san sunayen su ko basu sani ba.
4- Islama ta girmama hankali na kwa-kwalwa har ya kai matsayin da ya sanya shi babban alkali idan aka yi jayayya, game da imani, zamantakewa da halayen daidaikun mutane, ashe ke nan, an ba da hankali ne domin jin-jina masa kamar yadda ya cancanta.
5- Islama yayi kira ga kololuwar daidaito tsakanin mutane gaba daya, kuma ya kushe wa duk wata karkata dake nufin kawo wariya a tsakanin bil'adama, tare da fifita wani iri.

Yanzu 'yan'uwa maza da mata, ina fatan za ku karanta wannan dan littafin da kauna kuma zaku bashi kadan daga cikin lokutanku domin ku karanci jin kan Islama, domin a tsame bil'adama daga sabanin da ya taso ta hanyar wadanda suke kir-kiro karai-rayi akan islam ba tare da ilimi ba.

Muna maraba da tambayoyin ku game da Musulunci, kuma zamu ji dadin amsa kushewar ku matukar muna iyawa.

بِسمِ اللهِ الرحمنِ الرحيمِ {١}

اللّه لاَ إِلَـهَ إِلا هو الْحي الْقَيوم لاَ تَأْخُذُه سنَةٌ ولاَ نَوم لَه ما في السماوات وما في الأَرضِ من ذَا الذي يشْفَع عنْده إِلا بِإِذْنه يعلَم ما بين أَيديهِم وما خَلْفَهم ولاَ يحيطُون بِشَيء من علْمه إِلا بِما شَاء وسع كُرسيه السماوات والأَرض ولاَ يؤُوده حفْظُهما وهو الْعلي الْعظيم {٢٥٥}

Da sunan Allah, Mai rahama, Mai jin-kai

Allah babu abin bauta wa da gaskiya face Shi, Rayayye Tsayayye, gyangyadi baya kama Shi bare barci, abin dake cikin sammai da kasa duk na Sa ne, waye

wannan da zai yi ceto a wurin Sa? Face da iznin Sa, yana sanin abin dake gaba gare su da abin da ke bayan su, basu kewaye sani da wani abu na ilimin Sa face da abin da Ya ga dama, kujerarSa ta yalwaci sammai da kasa, amma duk da haka kiyaye su basu yi Masa nauyi Shine Madaukaki Mai girma. [Al-bakara-255].

**Manufofin mu**

Shine yada zaman lafiya a tsakanin mutane daban-daban, mu hada addinai gaba daya ta hanyar fahimta, domin yaki da kiyayya wace masu tsauraran ra'ayi suka haifar, yin aiki domin jin-dadin bil'adama gaba daya kuma da shiryar da karkatattun rayuka zuwa ga tafarki ma dai-daici da zai kai ga rayuwa ta jin-dadi mai gamsarwa.

Tsira da amincin Allah su tabbata a gareku.